Babu komai na Zakka akan Musulmi cikin dokinsa

Daga Abu Huraira - Allah ya yarda da shi -:zuwa ga Annabi : "Babu komai na Zakka akan Musulmi cikin dokinsa "
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Angina Zakka ne kan daidaito da kuma Adalci, don haka Allah ya wajabta ta cikin Dukiyoyin Mawadata kuma wacce take karuwa da kuma wacce aka tanada don juyawa, kamar abubuwan da suke futa daga cikin Kasa, da kayan siyarwa, kuma Dukiyar da bata Karuwa, wacce aka tanada don ajiya da Amfani to wannan babu zakka acikinta; don kebantarwar Musulmi don bukatar kansa: kuma kamar Abun Hawansa, Kamar Doki, da Rakumi, da Mota, kuma haka bawansa da ya tanada don yi masa Hidima da shimfidar sa da kwanuka da aka tanada don amfani sai dai antogace Zakkar fidda kai, to lallai cewa Ta wajaba kuma koda ba'a tanadi ta ba don kasuwanci, domin suna danfare da jiki ba da Dukiya ba.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/4519